# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na ɗaya: Mun dawo Kwalejin Zumunta

Wanda ya rubuta: Romie Singh
Wanda ya tace: Katrin Ogunsade, Naïma Guira
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Tafida: | ɗan shekara 17 |
| Dauda: | ɗan shekara 17 |
| Ɗanjuma: | ɗan shekara 16 |
| Layla: | 'yar shekara 16 |
| Saima: | 'yar shekara 16 |
| Malam Isma'ila: | ɗan shekara 43, baban Layla |
| Hassan: | ɗan shekara 12, ɗan'uwan Layla |

**MAI GABATARWA:**

Jama'a, barkanmu da saduwa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu", inda a yau za mu saurari kashi na farko daga cikin goma na wani sabon wasan kwaikwayo mai suna "Haɗin kan mutanen Sodangi", wanda a cikinsa za ku ji yadda addini da siyasa suka haddasa zaman doya da man ja tsakanin al'ummomi guda biyu, da kuma wasu maƙwabtan juna su biyu, da kuma tsakanin wasu matasa guda biyu da suke son juna. Amma wannan zaman doya da man jan ya hana su bayyana soyayyar da suke yi wa junansu. Bari mu saurari yadda waɗannan matasa suka fahimci muhimmancin tattaunawa da haɗin kai da haƙuri da juna wajen warware matsalolin da suka yi musu katutu.

A cikin wannan shiri na yau za mu saurari yadda ta kasance tsakanin Dauda da Layla da kuma abokan karatunsu. Waɗannan ɗalibai suna kan hanyarsu ne ta komawa makaranta bayan sun kammala hutunsu, kuma dukkansu suna shekara ta biyu ne a wata babbar kwaleji mai suna Kwalejin Zumunta.

Shi dai Dauda yana zaune ne a wajen kawunsa, wanda fada ne a wata cocin Katolika, sai dai ba ya jin daɗin zaman. Ita kuwa Layla hankalinta ya tashi saboda irin halayyar da ƙaninta ya fara nunawa. Ganin cewa an sami wani irin sauyin rayuwa a gidan nasu, sai ta fahimci cewa ya zama lalle ta taimaka wajen kula da shi. Sai ku ba mu aron kunnuwanku don ku saurari kashi na farko mai suna "Mun dawo Kwalejin Zumunta".

**Fitowa ta 1: A Kwalejin Zumunta**

Dauda, Tafida, Ɗanjuma

**MAI BA DA LABARI:**

Sodangi dai wani gari ne mai tashe a harkokin kasuwanci, wanda wani kogi ya ratsa ta cikinsa. A cikin wannan gari na Sodangi, akan noma masara da 'ya'yan itatuwa iri dabam-dabam. Tun shekaru aru-aru da suka shuɗe mutane suka ta yiwo hijira daga sassa dabam-dabam na Afirka zuwa wannan wuri saboda albarkar ƙasar noma ta wajen. Wannan ya sa wurin ya haɗa al'ummomi dabam-dabam waɗanda harshensu da al'adunsu da kuma

addinansu suka bambanta. Shekara goma da suka wuce wani shugaban al'umma wayayye a wannan gari na Sodangi, mai suna Sulaimanu Bahago, ya yi tunanin samar da wata al'umma ta 'yan Afrika tsantsa wadda za ta zamanto tsintsiya maɗaurinki ɗaya, ta hanyar kafa wata babbar kwaleji mai suna Kwalejin Zumunta. Fatan da yake shi ne wannan kwaleji za ta ƙunshi ɗalibai masu addinai dabam-dabam, maza da mata, 'yan shekara 16 zuwa 18. Shekaru biyu da suka shige ne Tafida da Dauda suka shiga wannan kwalejin. Kuma waɗannan abokai biyu na farin cikin sake haɗewa da sauran ɗalibai bayan hutun bazara da suka tafi.

**DAUDA:** A'a'a! Kai! Tafida, yaya kake?

**TAFIDA:** Kai! Amma fa na ji daɗin ganinka! Lafiya Dauda, kana lafiya?

**DAUDA:** Kome lafiya, ko da yake dai ka san zama da kawun nawa sai a hankali, ka san fada ne a coci!

**TAFIDA:** Gaskiya ne! Abin ai sai a hankali! Yaya sakamakon jarrabawarka kuwa?

**DAUDA:** To, bai kai naka kyau ba. Na san kai duk "A" ka samu.

**TAFIDA:** Haka ne! Babana ya yi farin ciki sosai, amma babata ko oho. Kai fa?

**DAUDA:** Na samu "A" huɗu da "B" uku. Iyayena da dangina a can ƙauyenmu duk sun yi farin ciki, sai dai gogan naka kawun nawa, ka san ba a iya masa! Ya cika ƙorafi! *… Kai Dauda, in ba ka mai da hankali ba sai yaron nan Tafida ya zama shugaban ɗalibai kana nan!*

**TAFIDA:** Wa, ni? Ai ba ni da farin jinin da zan iya zama shugaban ɗalibai!

**DAUDA:** Kai ɗin? Duk fa inda ka yi 'yan matan nan kallonka suke! Shi ya sa ni ma na maƙale maka!

**TAFIDA:** Ba shakka!

**DAUDA:** Haka za mu ci gaba da shagalinmu, mutumina! Za ma ka kai ni na ga irin ƙyale-ƙyalen cikin gari da kuma irin kyawawan 'yan matan nan naku na cikin gari, ko ba haka ba, mutumina?

**TAFIDA:** Ya yi daidai nawa, ban na sha!

**ƊANJUMA:** Kai! Ka ga maigidana Tafida, ina ka gane min Dauda kuwa!!

**TAFIDA da DAUDA:** A'a, Ɗanjuma, sannu da dawowa! Ashe kai ma ka dawo.

**ƊANJUMA:** Kai! Mu je a gwada ƙwanji mana!

**TAFIDA:** Ya yi Ɗanjuma nawa! Ka ga abokin fafatawata!

**ƊANJUMA:** A, to ban gane ba? Ni abokinka ne ko abokin fafatawarka? Wanne ka zaɓa?

**TAFIDA:** Kai, har an kaɗa komawa aji? Amma fa gayu na ji daɗin dawowarmu makaranta bayan hutun da muka sha.

**DAUDA:** Wai to ko mu ne Hasan da Hussaini da Gambon wannan kwalejin?

**TAFIDA da ƊANJUMA:** Mu ne mana! Allah ya daɗe da ran manyan yara na Kwalejin Zumunta.

**MAI BA DA LABARI:**
Su kuwa ɗin ne, don kuwa haka suke har a kulob ɗinsu na makaranta, Tafida da Dauda da Ɗanjuma, su ne manyan yaran Zumunta! A ɗaya gefen na makarantar kuwa, ga wata yarinya can kyakkyawa mai idanu, wadda Tafida ke yawan kallonta idan suna aji, wato Layla. Ga ta can ma tana gaisawa da ƙawayenta bayan komowa daga hutu.

**Fitowa ta 2: A kwalejin Zumunta**
Layla, Saima

**LAYLA:** La Saima! Kin ga yanda kika yi fes da ke! Da gani kin ji daɗin hutun nan.

**SAIMA:** Kai Layla! Ai ke ma haka. Kwarai kuwa, don kuwa mun je yawon shaƙatawa, sannan an sa da zumunci. Ai abin gwanin ban sha'awa!

**LAYLA:** Oohhh! To yaya, ba wani ɗan saurayi ne a gidan naku?

**SAIMA:** Layla ke nan! Ina ma dai a ce akwai! Duk samarin gidanmu kin ga yara ne! Ke kuma fa?

**LAYLA:** Kin san ni ɗan'uwan nan nawa matsala ne, kuma babana ya hana ni sakat, daga karatu sai aikin gida! Shi ba ya son wai rana ta dake ni dan kar in yi baƙi!

**SAIMA:** Kai! Wannan ai ra'ayin 'yan mazan jiya ne. Shi bai taɓa jin maganar nan da ake cewa baƙaƙen mutane ma kyawawa ba ne? Ina dai fatan har yanzu ba ki daina motsa jikin nan da kike yi ba.

**LAYLA:** A ɗaki nakan yi, saboda waje akwai zafi sosai, musamman idan mutum ya sa hijabi!

**SAIMA:** Kin ga Layla, ya kamata mu je mu ga yadda sauran 'yan mata Musulmi suke motsa jikinsu, tun da ba ke ce farau ba. Muna son ki zama a shirye don ki ƙara ciwo mana lambar zinari.

**LAYLA:** To! Ke da ma don na shiga gasa na ciwo muku lambar zinari kawai kike sona!

**SAIMA:** To ai kin san ita wannan Kwalejin ta Zumunta, makaranta ce da maza da mata kan haɗa kansu wajen harkokin wasanni. Don haka ki gaya wa babanki wannan yana daga cikin tsarin makarantar nan, kuma da ma abin da babarki take so ke nan.

**LAYLA:** E, gaskiyarki. Allah sarki, kin ga da tana nan da sai ta sa Hassan wata rana ya ziyarce ni, ko wannan rawar kan nasa ta ragu.

**SAIMA:** Haba Layla, ki kwantar da hankalinki! La, kin ji ma an kaɗa ƙararrawar *assembly*.

**Fitowa ta 3: A Kwalejin Zumunta**

**MAI BA DA LABARI:**
To a daidai lokacin da ake taken makaranta, haka ma kogin da ya ratsa garin nan yake gudana. Kuma kamar yadda ruwan kogin nan mai ƙasa-ƙasa ya ratsa garin nan, haka ya raba tsakanin gidajen wasu manyan mutane na garin: Wato gidan su Dauda, 'yan zuriyar Dambele, da kuma gidan su Layla, waɗanda su kuma 'yan zuriyar Umaru ne. Baban Dauda mai suna Maigida

Ranau Dembele dagaci ne a karkararsu. A wannan karkara ba wata makaranta ta a zo a gani, wanda a dalilin haka ne, kamar shekaru biyu da suka wuce ya yanke shawarar kai Dauda wajen ƙaninsa Fada Bana, don ya sa shi a babbar kwalejin nan ta Zumunta. Dauda yana kiransa cikin zolaya da Kawu Babban Fada. Abotar da ke tsakanin da shi da Ɗanjuma ta sa shi, Dauda, sha'awar rayuwar birni, kuma ya fahimci cewa ba wai karatu da zama cikakken Kirista su ne rayuwa kawai ba. Sai dai kuma Ɗanjuma ya hana shi sakat.

**Fitowa ta 4: A wani gidan abinci**

Dauda, Ɗanjuma, Tafida

**ƊANJUMA:** Kai gayu, wallahi ya kamata fa mu kama gabanmu!

**DAUDA:** Haba Ɗanjuma, kana gani fa yanzu muka fara holewa ni da Saratu, ɗan ba mu minti talatin mana!

**TAFIDA:** Mu ma nan ni da Rakiya, muna so a ɗan ɗaga mana ƙafa!

**ƊANJUMA:** Yanzu ku ko kunya ba kwa ji! Kai fa Dauda wata ran fada za ka zama! Kai ma kuma Tafida babanka fa babban ɗan jarida ne! Yanzu me za ku ce idan iyayenku suka gan ku a nan.

**DAUDA:** Haba! Mu fa karta kawai muke yi! Su ma da sun sami dama da sun ɗan taɓa fa!

**ƊANJUMA:** Kun ga, ni na tuƙo motar nan, in ba ku taso ba kwa taho da ƙafarku!

**DAUDA da TAFIDA:** A'a, tsaya! Tsaya Ɗanjuma!

**MAI BA DA LABARI:**

A halin da ake ciki kuma, a ɗaya tsallaken kogin, ga gidan su Layla can ana cin abincin dare. Nauyin kula da ita da ƙaninta Hassan yanzu ya dawo kan babansu ɗungurungum, saboda rasuwar da babarsu ta yi sakamakon wani ciwon kansa da ta sha fama da shi a 'yan kwanakin baya. Da ma shi shahararren ɗan kasuwa ne mai muƙami a wannan gari. Sai dai kuma yakan yi ƙorafin cewa, Fada Bana yana neman ya wuce gona da iri a harkokinsa a Sodangi. Don haka an fara samun rashin jituwa a tsakaninsu. Shi kuwa Hassan yanzu ya fara canzawa saboda irin huɗubobin da yakan ji daga manyan ɗalibai a makarantar Islamiyyar da ke masallacin da yake zuwa, wanda wannan yana ta da hankalin Layla.

**Fitowa ta 5: A gida**

Malam Isma'ila, Layla, Hassan

**MAL. ISMA'ILA:** Kin san wani abu kuwa, Layla. Ni ina ganin Fada Banan nan ya cika shisshigi. Na ga ya ƙwallafa ransa a kan filin nan da ƙungiyar Musulmi take so, amma kuma fa mu muka fara nema.

**LAYLA:** Me yake so ya yi da filin?

**HASSAN:** Akwai wani dalili ne da Kirista yake da shi in ban da ba ya son Musulunci.

**LAYLA:** Ka ga Hassan, mu ba irin wannan maganar muke a nan ba! Kai ɗan shekara goma sha biyu kawai, me ma ka sani a game addinin Musulunci ko na Kirista?

**HASSAN:** Ke dai ba kin je wannan shirmen Kwalejin Zumuntar ba, suna ta nuna muku cewa wai ba wani cikakken addini a duniyar nan da zai iya warware matsalar mutane. To in ba ki

sani ba akwai, domin ni ina zuwa makarantar Islamiyya kuma na san hakan!

**LAYLA:** To in haka ne ashe ke nan ka san cewa da Musulmi da Kirista sun yi imani da Allah ɗaya. Kuma mu Musulmi mun shaida cewa Annabi Isah (A.S.) shi ma manzo ne na Allah. Sannan kuma mahaifiyarsa Maryam baiwar Allah ce.

**HASSAN:** To ai kowa ya san Allah ɗaya ne. Allahu Akbar!

**MAL. ISMA'ILA:** Shhhh! Kai Hassan, yi mana shiru don Allah! … Ismai'la Umar ne ke magana. … E, ina ji. Alhamis sha ɗaya ga wata ko? … To shi ke nan ya yi daidai. Ina son na san lissafin daga wancan taron da muka yi. … Af kar na manta ka faɗa wa babban edita Malam Magaji. Don muna son jaridarsu ta *Muryar Sodangi* ta ɗauki rahoton.

**MAI BA DA LABARI:**

Saboda yawa da harkoki suka yi wa Malam Isma'ila, bai lura da irin sauyin halayyar ɗansa ba. Amma Layla tuni ta gano hakan, kuma tana hasashen abin da ya kamata a yi.

**MAI GABATARWA:**

Wannan shi ne ƙarshen shirin namu na yau! To a halin yanzu dai su Dauda, da Layla, da Tafida da sauran abokan karatunsu sun shiga sabuwar shekarar karatu. Amma kuma sam ba su san abin da za su tarar ba. Sai ku biyo mu zuwa kashi na biyu don ku ji yadda Tafida ya tunkari ƙalubalen da ya fara gamuwa da shi. In kuna son ku sake sauraron wannan shirin, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.